**Vol II No. 13**
**December 1999** **(Hausa)** **CHANGE Radio**

# Aiyukan Sadarwa.

KASAR HABASHA

**Ta Kaddamar Da Tashar Rediyo Na Zamani a Afrika Da Gabas ta Tsakiya** **3min. 9secs** **8**

*An sami sabuwar Tashar Rediyon C D Yanzu a Africa.*

**Hanyar Samun Labarai Sabuwa: Sabbin Dokokin Aiyukan Internet.** **1min 34 secs.** **7**

*Sabuwar Tashar Rediyo dake kan Hanya.*

TATTALIN ARZIKI.

**Tashar Tauraron Dan Adam zai iya samar da dala biliyan 50 a shekara ta 2000.** **1min. 38 secs** **7**

*Binciken sararin samaniya, kwalliya ta fara biya kudin sabulu*

ILMI.

**Kungiyar UNESCO ta kammala babban tarihin Afrika** **2mins 37sec.** **10**

*Aiyukan shekaru 35 na sake ganowa da kuma tsarawa kan gudunmawar Afrika ga harkokin tarihin Duniya.*

**Sabon bincike ya baiyana ainihin dalilan dake hana mutum yin karatu.** **2min. 22sec.** **4**

*Yaran da ba sa iya karatu saboda lalura, mai yiwuwa su sami ilmi tare da magani.*

KIWON LAFIYA.

**Yiwa Mata kaciya har yanzu ruwan dare ne a Najeriya.** **3min. 48secs.** **3**

*Sabon nazarin da akayi ya tabbatar har yanzu anayiwa mata kaciya a sassa daban-daban a Najeriya.*

**Kungiyara Najeriya ta sami kyauta ta Duniya kan ilmin jima'i.** **1min. 34 secs.** **6**

*Bayan kwashe shekaru masu yawa tana aiki kan ilmantar da jama'a game da jima'i a Najeriya, yanzu ta sami kyauta.*

**Cutar Kanjamau Har Yanzu Babbar Matsala Ce, Ganin an Kusa a Ranarakula da Cutar ta Duniya** **2min. 36secs.** **5**

*Koda shike Cutar Kanjamau babbar matsala ce a Duniya,kowani uku daga cikin hudu na masu cutar sun fito ne daga Afrika.*

TSARIN BIRANE

**Gyaran Gari da akeyi a Khartoum ya sanya dubban mutane sun rasa gidaje.** **2 min 14 secs.** **9**

*Birnin Khartoum na shan suka saboda ragayyara iyalai da dama.*

MATA

**Hukumar samar da canji CFC ta shirya wani Silma kan Matan da mazan su suka mutu.** **2mins. 15secs** **6**

*Irin matsalolin da Matan da mazajen su suka mutu ke fuskanta a Najeriya.*

# Yanayin Muhalli

GADUN YANAYI

| | | |
|---|---|---|
| **Ita tuwan da suak shekara dubu cikin littafi guda.** | **1min 33 secs.** | **5** |
| *Itacen da yafi tsayi a duniya har yanzu yana raye.* | | |

ILMI

| | | |
|---|---|---|
| **Yankin Neja Delta: Ana kara samun wayewar kai kan muhalli.** | **2mins 50 secs.** | **8** |
| *Kungiyar Rawya duniya tana aiki domin ilmantar da jama'a kan yanayin muhalli a yankunan Neja Delta.* | | |

SHARA

| | | |
|---|---|---|
| **Sabuwar hanyar kula da shara a kasar Argentina.** | **2 mins 7secs.** | **4** |
| *Wani gagaramin Birni a Argentina ya samo sabuwar dabarar sarrafa shara.* | | |

DABBOBIN DAWA:

| | | |
|---|---|---|
| **Sabuwar Dabara ta kara karfafa ilmin muhalli a kasar Ghana.** | **2 min 14sec.** | **9** |
| *An gano wau irin Nau'in Kwanta rafi da ake zato sun bace.* | | |
| **Wani Alkali a Amurka ya dakatar da sare itatuwan katako domin kare kifaye.** | **51 sec.** | **13** |
| *Wata kotun tarayyaz Amurka ta yanke shawarar kyautata wasu irin kifaye.* | | |

KIMIYYA:

| | | |
|---|---|---|
| **Wata sabuwar hanya ta gano cewar babu Teku a Duniyar Mars.** | **1 min 3sec.** | **14** |
| *Wata kila ba a taba samun teku ba a Duniyar Mars.* | | |

KASUWANCI.

| | | |
|---|---|---|
| **Sabuwar kawance domin yaki da bude kafofin kasuwanci.** | **1min 3sec.** | **14** |
| *Yaki da abokin gaba.* | | |


# Sashin Yara

| | | |
|---|---|---|
| **Dalilin da yasa 'ya'yan Chafali ke da hawaye a idanun su** | **4mins 49sec.** | **11** |
| *Tatsuniyar kabilar Zulu tayi bayani kan dalilin da yasa 'ya'yan Chafali ke da hawaye a fuskar su.* | | |
| **Tsawon yaushe ne mutum zai rayu bayan kasa ta sare shi** | **1 min 50sec.** | **11** |
| *Yaya dafin dake cikin sarar maciji kasa?* | | |
| **Kofar Ruwa** | **10min 55secs.** | **12** |
| *Kurege na zato yafi kowa wayo,sai dai kunkuru ;ya nuna masa ya fi shi.* | | |
| **Karin Maganar Muhalli.** | **51secs** | **14** |
| Ina dan Adam ke zuwa bayan ya bar duniya? | | |
| **Sau Nawa Kudan Zuba Ke Yin Zuma A Shekara?** | **1min 28sec.** | **14** |
| *Sau nawa itatuwa ke yin furanni a shekara?* | | |

# Labaru

**Har Yanzu A Nayiwa Mata Kaciya A A Najeriya. 3 Mins 48 Sec.**

Har yanzu ana gudanar da al'adar nan ta yiwa Meta Kaciya a wurare da dama a Najeria.Wannan kuwa an gano ne cikin biciken da aka gudanar a sassa daban daban, wanda kuma gidan Rediyon Najeriya ya gabatar cikin rahoton sa a watan Nuwamba, inda yace Gwammatin jihar Ogun ta haramta yiwa meta kaciya. Kowani daya cikin uku na ýan Najeriya da shekarun su ya kai 18 yayi naám kan cewar zai cigaba da yiwa ýar sa kaciya. Irin wadan nan mutanen sunfi yawa a sashin Yammacin Najeriya inda aka sami fiye da kashi 50 cikin dari a binciken, wadanda suka furta haken. Binciken da wani Kamfani dake Lagos ya gudanar kwanan nan watau RMS ya nuna cewar za a cigaba da wannan aládar har zuwa karni na gaba musamman a yammacin Kasar.

Kamfanin an RMS ya zanta da mutane dubu 5 wadanda shekarun su ya kama daga 18 cikin wasu manyan Kabilu Kasar 12 jihohi 36. Haka kuma ganawar anyi ta ne tsakanin mazauna birane da kauyuka kuma yawan maza da mata da aka tattauna da sun daidai ne. Sakamakon ganawar ya nuna kashi 70 cikin dari a yammacin Najeriya sunce anayiwa mata kaciya. A Lagos kashi 50 cikin dari, a Gabashin Najeriya Kashi arba 'in cikin dari yayinda a Arewacin Najeriya Kashi 20 cikin dari.

Anfi gano samfurin sosai idan aka bi tsakanin jihohi dakuma Kaliba, inda ake da Kashi 90 cikin dari na yiwa mata kaciya a jihohin Edo da Ondo da Bayelsa, dakuma kashi 80 cikin dari tsakanin kabilun Urhobo da Ijaw dakuma Edos. Kimanin kashi daya bisa hudu na wadanda aka gana dasu a duk fadin kasar sunce anyi musa kaciya. Daga yankuna kuwa mutum uku daga cikin hudu da aka yiwa tambaya a yammacin Najeriya sunce anyi musa kaciya, sashin gabashi dakuma Lagos mace daya daga cikin uku tace anyi mata kaciya yayinda a Arewacin Najeriya daya ne daga cikin mata goma ke cewa anyi mata kaciya.

Da take bayayi a lokacin ganawar Ms Margit Cleveland na kamfanin RMS tace dalilin dali da mutanen ke bayarwa sun sha bamban, saidai kusan dukkan su sunce sunayi ne saboda al 'ada tayiwa yara maza da mata kaciya a Najeriya. Wasu dalilan shine kaciyar tana hawa mata jaraba kuma tana taimaka musu yayinda suka zo haihuwa. Amma Ms Cleveland tace kaciya bata hana jaraba ga mata, domin akasarin mata karuwai duk anlyi musu kaciyar.

Kamfanin an RMS bai gano ba daga mutanen da ya gana dasu kan a binda suke daukar yiwa Meta kaciya a Najeriya. Koda yake binciken shine mafi sahihanci yazuwa yanzu a Najeriya Ms. Cleveland tace zata so gno wasu dalilan dake sanya akeyiwa Mata kaciya nan gaba.

Wadanda zasu hada da yiwa kananan kabilu intabiu wadanda ba ayiwa ba a wannan lokaci tare da ganawa da Meta kadai, tare da hadawa da wasu kasashen kamar su Camerou da Ghana ta yadda za a gano ainihin dalilan dake sanyawa akeyiwa Meta kaciya tare da same sahihan dabaru da hanyoyin da za abi wajen hanawa. In har ba ayi kokarin kawo karshen wannan al 'ada ba to kuwa zai cigaba ne har zuwa 'ya 'ya da jikoki masu zuwa nan gaba. Kuma ba za iya magance shi ba. Domin kuwa ba al 'ada bace da zata mutu da sauki inji Cleveland. *RMS.*

**Sabubuwar Dabarar Sarrafa Da Aka Fara A Kasar Argentina 2 mins 7secs**

Birnin Salta dake kasar Argentina dake da yawan mutane dubu dari biyar ya shiga sahun sauran manyan biranen duniya wadanda suke daukar sabbin dabarun zamani domin shawo kan shara.

Kwanan nan ne birnin dake samar da shara Tan metan da hamsin ya bullo da wani shiri mai karfi domin sarrafa sharar nan da shekaru 10masu zuwa. Babban abindake cikin shirin shine na maida dibar shara na kasuwanci inda ýan kasuwa zusu rika tafiyar da harkar kwasa da zubarwa. Za Agudanar da shirin ne bisa mataki-mataki har biyar wanda za afara da wayarwa da jama ‘a kai na tsawon shekara daya, tare da ilmantar da jama ‘a kan wannan sabuwar dabara. Kowane za a gudanar ne tsakanin shekara daya zuwa shekara uku.

Sauran matakan sun hada da hada da ahekaru biyu, wanda a lokacin kamfanonin ‘yan kasuwa zusu fara kwasar sharar kowace rana bayan da aka fara shirin kx gwaji. Sauran ragowar shekarun biya zasu kasance na tafiyar da irin ribar da aka samu kan shirin tare da tabbar da ganin akalla rabin birnin mazaunan sa na tara sharar su ta yadda zusu bambance tsakanin shara irin daban-daban misali shara irin kwalabe da karafa da takardu da robobi da sauran su ta yadda za asake sarrafa su domi yin amfani.

A rukinin karshe, wanda zai hada da shekaru na hudu da na biyar zai kasance kashi dari domin tara sharar da za asake sararafawa ne.
Wani kwarare kan harkar sharar Mr. LUcas Seghezzo, wanda yana cikin wannan shirin na birnin Salta yace birnin ya kuduri aniyar samun nasarar shirin.

Mr. Seghezze yace za akuma sa ido kan yadda za arika tafiyar da shirin baki daya domin tabbatar da sahihanci da nagarta dakuma bada kwazo.
*UWEP.*

**Sabon Bincike Ya Ganoni Ainihin Dalilin Dake Hana Iya kara Tu 2mins. 22secs.**

Sabon bincike ya nuna cewarwasu jijiyoyi sune ke sanya mutum ya kasa karatu in har basa aiki yadda yakamata. Mutane basa iya yin karatu koda kuwa suna da sha’awa dakuma damar yin karatun. In har wannan sakamakon gaskiya ne to kuwa zai tabatar d cewar mutm na cikn kasadar rashinyin karatu inji wani kwarare kn tatalin arziki. Kafin wannan lokaci masana halayyar jama’a suna zato cutar rashin iya karatu matsala ce ta daban. Sunyi imani cewar masu fama da irin wannan cutar suna faane da rashini ya fahimta abinda ake sara zasu karanta. Wannan zato kuwa ya tabbata ba gaskiya ba domin irin wadan nan mutane basa samun matsala wajen yin mu’amala da baki. Sabuwar hanvar gano irin wanman cuta yanzu ta nuna cewar rashin iya karatun na faruwa ne saboda rashin aiki yadda yakamata na wasu jijiyoyi dake kaiwa kwalwa. Wanna rashin aikin na kawo saibi wajen aikin karatu cikin hanzari,wanda ita kwalwa ke karba daga abinda idanu ke gani ko kunne ke ji. Inji John Gabriele da Torke. Klingberg na Jami’ar Stanford dake Amurka ne suka bull oda wannan sabuwar dabara ta cusawa irin na maganadisu (DTI).

Gano ita wanna cutar rashin iya karatu an gano ta ne ganin masu fama da ita suna fushantar wahaloli wajen ji. An gano cewar su irin wadan nan nutane basa iya karanta layukan rubutu wadanda suke da harufa kusan iri guda musamman in har suna bin juna ne cikin hanzari. Dr. Gabriele da Dr. Klingberg sunce binciken nasu ya gano iya karatu na tare da tafiyar sauti cikin jijiyoyin dake zuwa kwalwa ne. DTI wata hanya ce ta auna motsin ruwan dake cikin jijiyoyin jikin dan adam. Ta yin nazari kan irin saurin da ruwan keyi cikin jijiyoyi har zuwa kwakwalwa masana kimiyar sun gano cewar akwai ingantatun hanyoyin tafiyar ruwan sosai a jikin mutanen da basa fama da irin cutar hana iya karatun.
*The Economist*

**Cutar Kanjamu Babbar Matsalar Kuniya Ganin An Doso**
**Ranar Yaki Da Cutar Na Karatowa.** **2mins 36sec.**
Afrika ce ke sahun gaba wajen yawan mutanen da suka kamu da kwayoyin cutar kanjamau dakuma wadanda suke fama da cutar. Wanna kuwa na kunshe ne cikin rahoton da aka bayar kwanan nan daga majalisar Dinkin duniya. Gaga cikin mutane miliyan 34 dake fama da cutar ta HIV/AIDS a duniya kasashen dake yankin Afrika kadai dake fama da cutar sunkai miliyan 23. Cikin wata kasidar da majalisar dinkin duniyar ta buga kafin ranar yaki da cutar daya ga watan Disamba 1999, ta nuna cewar Afrika ce ke kan gaba da wadanlda ke fama de cutar. Kusan kowani mutumin da ya mutu a sanadiyar cutar. Kusan kowani mutumin da ya mutu a sanadiyar cutar da ake samu daga Mata a shekarar 1998 wadanda suka kamu da cutar ne. Daga cikin yara dubu dari shida da aka haifa da cutar ta kanjamau dubu dari biyar yaran Afrika ne kuma sune kashi 80 cikin dari na yaran dake mutuwa a sakamakon cutar a duniya. Kamar yadda kasidar da akayiwa lakani matakin majalisar dinkin duniya kan cutar kanjamau Afrika ce ke da Mata mafiyawa da suka kamu da cutar a duniya..

Koda shike Afrika itace cutar tafi yin kamari,duk da haka cutar batada iyaka tsakani nahiyoyi ko tsakanin kabila ko mukami. A yanzu haka akwai miliyoyin mutane dake fama da cutar a sassa daban na duniya. Wadanda suka hada ha mutane miliyan 7 a nahiyar Asia,kimanin miliyan biyu a Latin Amurka da miliyan daya da Arewacin Amurka da wasu dubban daruruwan a yankin Caribean da Turai da Gabas ta Tsakiya da Ausralia da New Zealand dakuma tsibiran Pacific. Babban sakataren majalisar dinkin duniya Kofi Anan yace tilas ne mu fahimtar da jama'a cewar wannan cutar babban baraz ace kuma tilas a hada karfi da karfe waje guda domin yaki da ita. Tilas ne duniya ta daura damara domin yaki da wanna mugunyar cutar da duniya baki daya.

Majalisar dinkin duniya tana saran duniya zata kuduri aniyar yaki da cutar a wannan ranar d aka kebe. Gaga cikin hanyoyin da ake sran bi domin yaki da cutar sun hada da kudurin shugabanin kasashe ta fuskar siyasa,da aiyukan hadin gwiwa tsakanin wadanda suke da sha'awa domin karya alkadarin cutar,tare da kara kudaden da ake bayarwa domin gudanar da bincike da samar da allurar da zata karya lagon cutar tare da kara yawan aiyukan da suka shafi matasa.
*HIV/AIDS MORE THAN A HEALTH CRISIS*

**Bishiyo Yin Shekara Dubu A Littafi Guda** **1min. 33sec.**
Rannar 24 ga watan Nuwamba a London hukumar kare gandun daji ta duniya WWF zata kaddamar da gagarumin yekuwa kan wani littafi dake kunshe da wasu bishiyoyi da suka dade a duniya,wadanda ake kyautata zato sun shekara dubu a duniya,sun kuma kunshi iri daban-daban har ashirin da biyar. Haka kuma littafin ya kunshi wasu ;sabbin tsirrai da aka gano cikin wannan zamani. Littafin da ake kira Littafin karni na bishiyoyi,tsoffin bishiyoyin wani madaukin hoto mai suna Edward Perkar da Anna Lewing ne suka hada shi. Shi Parker yayi yawi a wurare dama a duniya na tsawon shekaru yana daukar hotunan bishiyoyi a dazuzzuka.

Bayanan tsoffin iyatuwa,da ya kunshi irin bishiyoyi daban-daban a duniya dakuma irin bayanan su,da al'adun su da tarihin su dakuma yanayin su,ciki harda irin girman su da tsayi da shedaru ciki harda bishiyar da tafi tsufa a duniya.. Akwai ma bishiyoyin da aka dauko daga yankunan dazuzzukan yankin nan mai zafi na Amazon da yankunan arid dake hamadar Namib. Dd' yake baiyana tsoffin bishiyoyi da cewa abin mamaki ne kuma littafi mai kyau,wani mai harsashe yace ya hade da ;wasu hotun mafiya kyanu da Mr. Parker ya dauka ana iya sautun littafin daga Sonia Pugh dake Collins da masu buga litattafai na Brown dake kasar Biritaniya (Tel+44171924 2575)
*WWF.*

**Wata Kungiya A Najeriya Ta Sami Kyau Ta Ta Duniya:**
**Kan Il min Jimai 1min. 34sec.**

Wata kungiya mai zaman kanta da ake kira kungiyar sha yanzu magani yanzu kan kiwon lafiya (AHI) wanda ta shahara kan aiyukan ilmantar da jama'a game da jima't ta sami kyautar WAS ta shekarar 1999. Kyautar kungiyar kula lda ilmin jima'i ta duniya WAS ce ta baiwa kungiyar a Hong Kong a taron ta na 14 da akayi cikin watan Agusta. An zabi kungiyar ta Najeriya ne bisa shawarar da kwamitin da kungiyar ta WAS ta kafa yayi nazarin kungiyoyin da aka gabatar da sunayen su.

Da yake gabatar da kyautar Dr. Eli Coleman shugaban kungiyar ya baiyana muhimmancin ta Ana bada kyautar ne ga kungiyar da tayi fice ainun wajen ilmantar da abubuwan da suka shafi jima'i a kasar su ta hanyar shirye-shirye masu gamsarwa,kuma ana bada kyautar ne da nufin karfafa gwiwa ga sauran kuingiyoyi na duniya domin suma su bada himma. Kyautar ta zo a matsayin ba zato ga kungiyar ta Najeriya,wanda ta taka muhimmiyar rawa wajen shirya ka'idoji kan sahihan aiyukan ilmi kan jima'i a Nairiya. Ba ma saran samun wannan kyautar inji wani jami'in kungiyar Dr. Uwem Esiet yayinda yake karbar kyautar a madadin kungiyar. Yace kyautar zata karfafawa kungiyar gwiwa wajen cigaba da aiyukan kara kyautata rayuwar matasa ta hanyar gudanar da ilmin jima'i a Najeriya.
*Growing Up*

**Hukumar Kyautata Muhalli CFC Ta Kaddamar Da Silma Kan**
**Matan Da Mazan Su Suka Mutu 2mins 15sec.**

Za a kaddamar da wani hoton silma na tsawon mintoci 30 kan irin halin da Matqan da mazan su ka mutu suke ciki a Najeriya a wau sassa uku cikin wannan watan. Silman da adayiwa lakanin MUTUWA KA RABA, an dauko shine a sashin gabashin Nageriya inda nan ne matsalar tafi kamari kana taki jin magani. Za a kaddamar da silman ne a lagos,da Enugu dakuma Patakwal tsakanin 29 ga watan Nuwamba zuwa 8 ga watan Desamba. Hukumar ta CFC ta shirya silman ne a bara domin baaiyana irin wannan hali ta al'adaa.

Silman yayi tsokaci kan irin tattaunawar da akayi da irin wadan nan Matan da suka rasa mazajen su,da wakilan kungiyaar irin wadan nan Matan da sauran jama'a,wadanda ke taimakawa wajen sauwakawa irin wadan nan Matan wahalolon da suke fuskan ta. Da yawa daga cikin su,sun sami sukunin baiyana irin abinda ke damun su a zuciya da irin halin da suke ciki da bakar wahalar da suke sha na tsawon shekaru. Lallai ya tabo irin sukurkucewar da burin su yayi a rayuwar su. Mutuwa ka rabaA ya tabo irin yadda al'adu suka jefa irin wadan nan Mata cikin tasku.

Wadanda suka hada da zaman takaba na lokaci mai tsawo,da sa Matan su aske kan su dakuma sanya su yin kuka mai tsanani ta yadda zasu wanke kan su daga zargin ko sune suka kashe mazajen nasu tare da yin wasu tsatsube-tsatsube domin kauda fatalwar Mazajen su da suka mutu. CFC ta shirya silman ne tare da taimakon hukumat talabijin mai kula da harkokin yanayi dake kasar Biritaniya (TVE),wanda ke samun kudaden sa daga kungiyar tarayyar Turai.
*OBASI OGBONNAYA.*

**Tauraron Dan Adam Samar Da Dala Biliyan 50 A Shekara Ta 2000** **1min 38sec.**

Kusan shekaru arba'in da akayi ana bincike kan sararin samniya kwalliya ta fara biyan kudin sabulu ta fuskan samr da makudan kudi da fasaha ga kasasshen da suka fara tafiyar da sikin na turai da Amurka. Kimanin dalar biliyan 36 aka samu ta fuskar kaswuwanci kan tasoshn tauraron dan adam da wasu sauran taurarin na dan adam a bara. Haka kuma an sami karuwa kan harkokin fasaha wanda ake saran kasashe masu tasowa suma zasu amfana. Wannaan kuwa na kunshe ne cikin taro na uku kan biciken sararin samaniya da aiki da abubuwan dake sararin samaniya (UNISP) da akayi a Vienna cikin watan Yuli. Kamar yadda taron na UNISP 111 yaayi bayani an kiyasta samun dala biliyan 50 cikin shekara ta 2000. Waannaan ya nuna karuwa kan abinda za asaamu na aiyukaan binciken sararin kamr yadda yaake ga taron na Vienna kan yadda dan adam zai aamfana daga sararin samaniyya.

Daga cikin batutuwan da aka zartar a taron na Vienna sun hada da shirin kare yanayin sararin samaniya tare da albarkatun dake akwai domin amfanin tsaro da zamantakewar bil-adama. Shirin an ruwaito cigaba ne kan shirye-shiryen da akayi tunda farko a tarukaan da akayi ashekarar 1968 dakuma 1982.Tattaunawar ta Vienna ta hada da taimakawa kaan harkokin fasaha da ilmi domin kasashe masu tasowa suma su ci gajiyar fasahar. Gajiyar sun hada ta fannin aikin gonayanayin muhalli tare da kare aukuwar haddurar kasa. Haka kuma samun aiki da na 'urar Internet ta hanyar tauraron dan adam a wuraren da ba a dasu domin bunkasa harkokin masana 'antu.

*Development Update*

**Hanyar Samun Laa Barai: Bisa Dokokin Internet** **1min. 34secs**

Yanzu kana iya kama shirye-shiryen gidajen rediyo daga ko ina a duniya ta hanya yin amfani da na 'urar kkummputa. Wani babban kamfani dake Amurka daake samar da Internet ta hanyar Biznes On line. Com, ne ya sanya shirin ya samu ta hanyar kaddamar dda irin wannaan tashar rediyon na farko a A duniya a kasar Amurka. Ana iya samun ttashar yanzu ta hanyar (htt://www. the publicradiostation. com) wanda ke gabatar da shirye-shirye da dama a duk fadin Amurka da sauran duniya. Sun hada da jazz, da rahoto kan kayayyaki, da wakoki da shirin Mata da yanaayi da labarai da sharfi. Sashin aiyukan web ya maida hankali ne kan masu kanana da matsakaitan masana 'antu dake Amurka.

Da yin aiki da na 'urar internet dokokin suna canjawa daga tasha zuwa tasha inji Mr. E Munro babban jami 'in BiznesOnline, yace yanzu haka muna aiki da tasoshin rediyo da dama da talabijin da kamfanonin jaridu domin taimaka musu ta yin aiki da internet kamar fadada kafofin su. Hakka kuma Munro yace anyi ttsare-tsaren shirruka ta yadda mai sauraro zai san lokacin shirin da yake bukata ya saurara. Akwai kuma karin karfafa gwiwa,. In mai sauraro ya rasa jin wani shiri yana iya samu ta hanyar nema a rumbun adana shirruka. Kusan dukkan kafofin yada labarai irin su jarida rediyo da talabijin suna amfani da internet yanzu domin fadada kafofin su. Ta hanyar taba na úrar za ka kalli shirye-shiryen da kake bukata ta talabijin da karanta labarai ta jarida ko ka bude tashar rediyo domin jin shirin. Wannan tashar ita ta farko da za a iya samun ta kan layi.

*PR NEWSWIRE.*

# Sharhi.

**Ana Samin Karuwar Kula Da Muhallia Yankin Neja Delta: 2mins 50sec.**

Wata kungiya a Najeriya mai zaman kanta dake kare muhalli (LWNF) a karon farko ttana baiwa mazauna karkara damar baiyana ra 'ayin su a yankin Neja Delta ta wasu aiyuka. Aiyukaan sun hada da shirin gidaan rediyo kaan muhalli da tattaunawa a harshen turancin pijin da cikakken turanci da mazauna karkara, da wasanin kwaikwayo kan irin halin rayuwar jama ' a ta yau da kullum dakuma hotunan da ake likawa kan yadda jams 'a zasuyi mu ' amala cikin yanayiin da suke. Wadanda suke cin moriyar shirin sun hada da al 'umomindake zaune a Akipelai, da oloibiri da Biseni da ya kunshi kauyuka takwas.

Aiyukan da aka fara a watan Nuwaambar 1998 ya sami gagrumin karbuwa ga jama 'a . Ba-saraken Akipeloi ya gamsu bayan ganin shirin wasan kwaikwayo, wanda shine irin sa na farko da aka tabayi a kauyeen. A karshen wasan kwaikwayo, wanda shine irin sa na farko da aka tabayi a kauyen. A karshen wasan anji yana cewa 'lallaai yanzu ne naga kauye na ta cikin madubi '. Kungiyar ta kuma kara da taimakawa kauyawan wajen kafa kungiyoyin wasan kwaikwayo nasu da ake kira 'Odion ioobebh'kusan dukkaan kauyuka uku dake ankin suna da kungiyoyin wasan kwaikwayo nasu na kansu.

Wasu ashirruka biya na rediyo mai warka 13 da akayiwa taken lokaci yayi me ke faruwa ana gudanar dasu a tasoshin rediyoon jihohn Bayelsa, da Rivers dakuma Cross River da jihar Delta. Da yaake baiyana ra 'ayin sa bayan sauraron shirin na rediyo Cif Amakime Ogu basaraken Amananowei dake Biseni yace: 'Wannan shine abu mafi muhimmaaci da ya faru da mu, shirin ba kawai yanuna mana haaske ba ya kara fiddo da matsalolin da al 'umomin mu ke fuskan ta ga duniya'. Wata budurwa a Akipelai tace hirar na rediyo shine na farko da wata Mace akauyukan Bayelsa suka sami damar fadar ra 'ayiin su a baiyane.' Shugaban hukumar kare muhalli da tsare-tsare ta jihar Bayelsa Mr. Aureol D.Vainana yace hukumar sa ta yaba bisa amfani da rediyo da akeyi na wayarwa da jama 'a kai kan harkkokin muhalli. Ta hanyar shirukan rediyo kungiyar zata iya hada al 'umomi kan yadda zasu kawo canji game da yanayin muhalli. Yayi alkawarin cewar rediyon jihar Bayelsa zai rungum shirin da zarar ya fara aiki. Koda shike shirin ya kara wayarwa da jama 'ar yankin kai kuma ya sanu karbuwa har yanzu ba za afayyace yadda aka sa gaba ba.

*Living Earth/Nig. Foundation*

**Habasha Ta Kaddamar Da Rediyo Irin Na Zamani Domin Afrika Da Gabas Ta Tsakiya 3min 9sec**

kashen Afrika ta yamma zasu fara sauraron shirin gidan rediyo rangadadau daga kko ina cikin yankin kafin shekara ta 2000 ta hanyar amfani da rediyo na musamman da aka yi domin karbar shirye-shirye ta tauraron dan adam. Wannan kuwa ta hanyar kamfanin rediyo mai aiki da dijital da aka kafa domin saamar da shirrukan rediyo bai daya a likaci guda. Kamfanin cikin watan jiya ya kaddamar da aiyukan rediyo irin sa na farko dake amfani ds fasahar zamani, domin tabbatar da ingancin sauti a yankunan karkara inda ba asamu kama tasoshine rediyo a nahiyar Afrika, inda za afara da kasasheen Najeriya da Ghana da Senegal da Afrrika ta kudu, da Keenya da Cote D 'Ivoire da Masar dakuma Morocco.Ana karfafa shirin ne ta dakin wastsa labarai dake London da Washington zuwa Afrika ta hanyar amfani da karfin hasken rana da aka kaddamar a farkon wannan shekara. Shi wannaan rediyoon da ake kira AfriStar zai samar da labarai ta hanyoyi 25 da wake-wake da nishadantarwa da ilmantarwa a yankin da yakai kilomita miliyan 42 murabba 'i a Afrika da Gabas ta tsakiya. Wannan wata rana ce mai cike da tarihi a fannin rediyo inji shuggaban kamfanin na World space Mr. Noah Samara a wajen kaddaamar da tsarin na shekaru 1l0. A karon farko ya yaankunan da ada basa samun sauraron shirin rediyon duniya, ta dijittal. Shirin rediyon zai kai ga masu sauraro miliyan dubu ddaya a duniya.

Ana bukatar akwati rediyo na musamman da akayi m ai eriyaal kama tauraron daan adam ta hasken rana kafin sauraron shirin na AfriStar. Kimanin akwatunan rediyo dubu 30 ne kamfanonin rediyo na Hitachi, da JVC dda panasonic da Sanyo suka kera nnan da Disamba kimain irin wadan nan rediyon dubu 130 ne za a kera a saidawa kasasheen Afrika. Koda shike za a kera miliyoyin irin wadan nan rediyon domin saidawa mazauna karkaran Afrika bisa dan takadirin farashi a matsayiin makamin cigaba. Daga cikin aiyukan da kamfain keyi harda damar zaben shirye-shirye labaru daga tasoshin rediyo na kasa dana duniya da shirye-shirye cikin harsuna ciki harda turanci da faransanci, da larabci da Afrikaan. Akwai kuma shirin da AfriStar keyi na kaddamar da tshar AmerStar danufin kaiwa ga dukkaan bangrorin dake baya wajen samun ahirukan rediyio, a akalyi.
*PRNNEWSWIRE.*

**Gano Wata Dabba Da Akayi A Ghana Ya Sanya An Tashi Tsaye Wajen Kare Muhalli** **2min 14sec**

Gano wata irin nau 'in barewa da akayi kwanan nan mai suna sitatunga ya sanya an tashi tsaye wajen yekuwar kare muhalli a kasar Ghana. Ita wannan nau'in barewar sititanga ana samun ta ne a bakin rafi da yankunan dake da ruw ko koramai a gabashi dakuma kudancin afrika dakuma Najeriya. Ita wannan dabba ta bace baki daya a kasashen Africa irin su Cote d'Ivoire da Saliyo da Liberia da Senegal dakuma Gambia saboda farautar su da akeyi. Kafin wannan lokaci ita wannan dabbar ana zato ta kare a Ghana na. Amma kokarin da akayi na shata yankunan yawon dude ido a yankin gabashin kasar ne yakai ga gano ita wannan nau'in barewar a harshen tekun Avu. Wani jami'in yankin mai kula da yawon bude ido Mr. Frank Kofigah ne ya gano ta.

Ma'aikatar kula da dabobin dawa, da cibiyar bincike kan hallitu (NCRE) da hukumar kula da aiyukan yankuna masu ruwa ta Ghana sun baiyana sha'awar su ainun bisa gano dabbar da akayi. Sititunga da dabba ce da ake kauna a yankin na Avu. Yanzu basaraken yankin ya kafa dokar haramta farautar ta. Maatuka dai muna kaare ita wannan dabba a yankunan mu dabobin zasu cigaba da janyo hankalin masu yawon bude ido. Sauran kokarin da akeyi sun hada da kare wuraren da dabbobin suke. Jami'in kula da aiyuka a wurare masu ruwa na Ghana Mr. David Kpella yayi magana kan shirin da akeyi na yekuwar kare muhalli ga jama'a bisa cewar z a samu amfani fiye da yadda ake zato ta fuskar masu yawon bude ido fiye da yanka irin wadan nan dabbobin domin nama . Baya ga haka ma'aikatar kula da dabbobin dawa ta shirya sanya kungiyoyin kare muhalli na duniya cikin shirin yekuwar kare muhalli.
*Edward Ameyibor.*

**Gyarar Fuskar Da Akeyiwa Birnin Khartoum Ya Sanya Dubban Mutane Sun Rasa Gidajen Su** **2mins 14sec.**

Wani yunkurin da akeyi na yiwa birnin Khaurtoum gyarar fuska a kasar Sudan ya jefa dubban jama'a cikin rashin matsuguni. Wani jigo a kungyar kare hakkin dan adam ta Sudan,da ta kunshi 'yan jaridu da lauyoyi da malaman makarantu tace kokarin da akeyi na kauda masu karamin karfi daga birnin domin gina manyan hanyoyi da wuraren ajiye motoci ya tilastawa mutane dubu 40 rasa gidajen su. Wadan nan mutanen sun bi sahun mutane miliyan uku da tuntuni suke zaune a bukkoki da unguwanin marasa galihu dake kewayen birnin,inda suke zaman gudun hijira bayan da suka tserewa yakin basasar kasar na tsawon shekaru 16.

Aikin wanda Gwamnatin Khartoum ke gudanarwa tun shekarar 1998 ya sanya an ruguje gidaje akalla dubu metan duk na masu karamin karfi. Shugaban kungiyar kare hakkin dan adan na Sudan Ghazi Suleiman yayi kukan cewa wadanda aikun ya tayar sun koma wuraren dake nesa da wuraren samun aiki,da makarantu dakuma wuraren ibada dana kiwon lafiya. Duk da haka Gwamnati tace iyalan da abin ya shafa an basu filaye a yankunan da suka zaba,yanzu haka suna more rayuwar su. Gyarar fuskar da akeyiwa Khartoum ba yana nufin fidda mutane daga gidajen su da karfin tsiya bane inji wani jami'in gwamnatin Sudan.

Gwamnan birnin Khartaum Mazoub al Khalifa ya bada sanarwa kwanan nan cewar Gwamnatin sa tana shirin gyaran birnin danufin inganta shi irin na zamani a Afrika. Khartoum zai zama birni mafi kayatarwa a Afrika in har shirin ya sami isasun kudi. Kamar yadda Gwamnan yace birnin da aka kafa shekaru dari,danufin mazauna miliyan biyu yanzu akwai mutane sama da miliyan 6,ciki harda mutane miliyan uku da yakin basasa ya yagayyara daga kudancin Sudan. Al Khalifa yace dubban iyalai ne za a tsugunar da su a sabon wuri domin gina hanyoyi da wuraren ajiye motoci. A bara gwamnatin kasar ta kirkiro da hukuma da ake kirar hukumar raya birnin Khartoum (KSDA) domin sa ido kan gudanar da aikin gyarar fuskar,da biyan diya ga iyalan da aikin ya tayar.
*IPS.*

**Kungiyar UNESCO Ta Kamammala Aikin Rubuta Tarihin Afrika** **2 mins 37sec.**

An buga rukunin karshe na babban litafin tarihin Afrika,wanda kuma yakawo karshen aikin da kungiyar UNESCO ta fara tun shekarar 1964,domin tara bayanai da aiyukan tarihin hahiyar Afrika tun zamanin jahiliya har zuwa yau. An tafiyar da aikin ne da nufin gyara daukar da akeyi na cewar aiyukan kimiyan Afrika basu da tarihi kuma basa iya kawo cigaba in ba hada da wasu aiyuka na wajen Afrika ba irin su aikin soja da na zamantakewa dakuma al'adu. Kowani daya daga cikin rukuni takwas na litafin yayi magana kan irin gudunmawar da Afrika ta bayar ga cigaban dan adam ciki harda aiyukan karafa,da aikin gona dakuma dadadiyar fasahar nan ta kasar Masar. Haka kumakulitafin ya nuna cewar mutum daya ke ke rayuwa daga cikin kowani mutum hudu da aka saida a matsayin bayi yayinda ake ketare teku dasu zuwa aikin bauta. Rukuni na takwas na littafin an gabatar dashi ne a Trabulus cikin watan Mayu domin kawo karshen aikin na tsawon shekaru 35.

Babban taron UNESCO na 1964 ne aka kaddamar da aikin littafin a Paris yayinda aka tsaaida shawarar tattaunawa tsakanin al'adu daban-daban na duniya,domin mutane ba baan-daban zasu bada ra'ayin su kan fahimtar juna. Sabbin kasashen Afrika da suka sami mulkin kai dana Aasia na bukatar tabbatar da al'adun su ga duniya tare da gyara su dakuma asan su sosai. Kamar yadda kuddurin aikin ya nuna Afrika na bukatar gyara kura-kuran dake akwai na na cewa Afrika bata da wani abin tarihin azo agani. An gudanar da aikin ne bisa matakai da dama. Na farkon shekaru biyar 1965 zuwa 1970 anyi amfani dasu ne wajen bincike kan asalin tarihin Afrika. An samu ne kuwa daga kunnen ya girmi kaka,da wuraren adana kayan tarihi da kayan tarihi na karkashin kasa.

Rukuni na biyu 1970 zuwa 1980 aka bullo da dabarun rubuta tarihin,wanda ya haka da kafa kwamiti mai karfi na kasa domin sa ido kan aikin baki daya. Kashi daya bisa uku na wakilan kwamitin mai wakilai 39 na 'yan Afrika ba ne,sun fito ne daga Amurka da Biritaniya,da Brazil dakuma Carebean. Tsarin aikin ya bada shirya hotuna da sauran aiyukan zane-zane,an kuma nada mawallafa fanoni daban-daban na aikin dakuma darekto ga kowani rukuni. An fara buga littatafan ne a she karar 1980. An sami jinkiri wajen kammala wanna matakin saboda rashin kudi,biyowa bayan fitar Amurka da wasu kasashe daga cikin kungiyar ta UNESCO a shekarar 1990.

Rukuni na takwas yayi magana kan Afrika na wanna zamani. Darektan wanna rukuni kuwa wani shahararen masanin tarihin anan ne dake zaune a amurka dan kasar Kenya Farfesa Ali Mazrui. Aiki ne mai muhimmanci da yayi nazari ainun wanda ya kauda mulkin mallaka ya sake tsarin nahiyar tare da kyautata matsalolin ta dakuma dangantakar ta da sauran kasashen duniya inji Christopher Wondji wani babban jami'in aikin. Mr. Wondji yace babban takaicin sa shine aikin bai hada da abubuwan da suka faru a shekarun 1990 ba.

*The Courier*

## Sashin Yaraa

**Tsawon Yaushe Zakar Rayu Bayan Kasa Ta Sare Ka? 1 min 50secs.**

Wannan babbar tambaya ce mai wuyar amsawa saboda watakila ba zaka mutu ba in kasa ta sare ka. Kasa macijiya ce dake da dafi,in har tayi sara ta kan sanya dafin cikin jikin wanda ta sara. Abinda kasa take kashewa sune tsuntsaye da wasu kananan dabbobi irin su bera. Bata cika damuwa da mutane ba,domin haka mu bama cikin abinda take ci. Kasa tana saran mutane ne in har suka tsorata ta,kana tana kokarin kare kanta. Takan saka dafi kadan ne ko ba ba ta sakawa in har ta sari mutum. In har dafi ya shiga cikin jikin ka ya kan sanya mutun yayi rashin lafiya domin haka zai bukaci samun magani a asibiti. Koda bata saka ma dafi ba ciwon da sarar zaiyi ma na iya ruruwa saboda dattin da zai shiga na hakoran ta. Masana kimiya da sukayi nazari kan macizai sunce akasarin mutanen dake mutuwa saboda saran maciji suna mutuwa ne saboda tsoro bawai saboda dafin ta ba. Akwai kasa iri-iri daya daga cikin su itace kasan Masar. Wanda take son zama a shuri. In ta fusata sai ta daga jelar ta wanda ke da kugiya. Wani lokutan kacizai sukanyi likimo kamar sun mutu. Amma mutanen da su kasan maciji sosai suka san halayyar su basa ta ba su koda a mace ko a raye ne.

*Chongololo*

**Dalilin da Yasa 'Ya'yan Cafalike Da Hawaye A Fuska 4mins 49sec.**

A wani zamani anyi wani mugu kuma malalacin maharbi,wata rana zaune a gindin bishiya dake tudu yana kallon garken wasu namun dawa suna tafiya suna kiwo cikin kwanciyar hankali,. Domin haka shi maharbin bai ma damu da ya tashi domin farautar su ba,domin bai son wahalar da kan sa cikin daji. Can sai yaji motsi cikin ciyayi ta dama dashi. Ashe wata damisa ce ke kwanto tana jan ciki a hankali domin farautar daya daga cikin wasan nana namun dawan dake tafiya cikin garke. Damisar tans sanda tana dada matsowa kusa da su wadan nan dabbobin. A hankali a hanali kana tana kokarin boye kanta. Shi wannan maharbin lyana nan yaana kallon duk abinda ke gudana, daga cikin dabbobin da lya bar garken shine damisar take fako wajen wannan hari na ta. Nan da nan sai tayi wani irin kukan kura ta aukawa wannaan dabbar da gudu kuma da karfin tsiya to kamo ta. Daga nan sai damisar ta dauko wannan dabbar da ta kama zuwa wata inuwa cikin ciyayi. Shi kuwa wannan maharbin yana nan cikin al 'ajabi da mamakin irin wannan hanzari da karfi da damisar tayi amfani dasu wajen kama wannan dabbar. A yayinda yake kallon ta sai kuma yaga ashe tana da wasu 'ya'ya guda uku kyawawa ita damisar wasaanda suka jiran ta a inuwar.

Daga nan sai kuma maharibin ya fara tunanin kko zai dauke wadan nan 'ya 'yaan damisar domin ta haka yake gani shima zaiyi nasara kamar yadda uwar tasu tayi nasara kan wannan dabbar da ta kama. Domin haka sai lya shirya mugunta a zuciyar sa, yana sane da cewar damisa bata tsare mutum, domin haka sai ya shirya cewa zai dauke daya daga cikin 'ya 'yan tan nan uku ya kowa masa yadda zai rika yi masa farauta. Sabode haka sai ya shirya har yazuwa lkacin da damisar zata bar wurin da 'ya 'yan nata suke. Yayinda rana ke faduwa sai damisar ta bar 'ya 'yan nata a wannan wurin ta tafi domi neman ruwan sha. Ganin haka sai wannan malalacin maharbin ya dauki mashin sa ya nufin wurin da 'ya 'yaan damisar suke. A nan ne yagan su guda uku kanana ko gudu ba sa iyawa. Bai yanke shawara ko wanne daga cikin su zai dauka ba, can sai yace gara ya dauke su duka uku domin yafi kan ya dauki daya.

Yayinda damisar ta komo bayan minti 30 sai ta iske an sace ‘ya ‘yan nata duka uku. Sai fa ta fara kuka tun cikin daren har washe gari kuka takeyi na rashin ‘ya ‘yanta kuma tana kukan ne da karfi ta yadda mutanen dake zaune a kauyen dake kusa kuk suna jin ta, sai wani tsoho yazo domin ganin abinda ya same ta. Allaah Ya sa shi wannan tsoho yana da hikimar zaman duniya yana kuma da ilmin dabbobi tare da kaunar su. Yayinda lya ga abinda ya faru, sai yayi fushi ainun, bawai kawai malalacin maharbin yayi satan ‘ya ‘yan ta ba har ma ya karya dokokin farauta da suka shinfida a tsakanin kabilar. Kowa na sane cewar maharbi tilas ne yayi amfani da karfin sa wajen yin farauta, amma ba daukar kananan dabbobi ba, kum,a duk wanda ya karya wannan ka ‘ida za a hore shi. Sai tsohon ya kooma kauyen ya shaidawa sauran dattawan kauyen irin abinda ya faru. Sai mutanen kauyen suka fusata, sai suka je suka sami malalacin maharbin suka fatattake shi daga kauyen baki daya, bayan sun kwace ‘ ya ýan damisar.

Suka daukko ‘ya ‘yan daamisar suka maidawa da ita damisar. Amma saboda tsananin kukan da damisar tayi-taayi hawaye sukayi da zubo mata, shine ya sa yanzu haka in kaga damisa za kaga fuskar ta akwai jiwayen hawaye a idon ta. Domin haka har kwanan gobe kabilar Zulu dake Afrika ta kudu, sun dauka cewar hawayen dake fuskar damisa, ta barli ne domin tuna mata irin kukan da tayi saboda rashin ‘ya ‘yan ta da malalacin maharbi ya sace mata.

*When Hippo Was Hairy*

**Rijiya** **10mins 55sec.**

Fari babban ma tsala ce. Yayi tsanani ta yadda dukkan dabbobi suna ji suna gani duk wuraren da suke samun ruwa suka bushe daya-bayan-daya. Yayinda dabbobin suka ga cewar tsakanin lokacin da fadamar su ta karshe ta bushe yazuwa lokacin faduwar damua akwai lokaci mai tsawo, sai suka shawar ta yin wani abu. Domin haka sai suka kira taron da kowani dalya daga cikin nau ‘in dabbobin zai halar ta domin bada shawara kan abinda za ‘ayi. A ranar taron sai dabbobin suka taru suka tattauna inda suka yanke shawarar su hada kai tare domin gina rijiyar da zasu rika samun ruwan sha. Sunce rijiyar tilas tayi zurfi domin gudun kada ta kafe in har farin yayi tsanani cikin ‘yan shekarun nan. Kowace dabba zatayi bakin kokarin ta wajen aikin gina rijiyar kuma ruwan kowai zai samu ne daidai-wa-daida.

Domin dabbobin na matukar bukatar ruwa sai basu bata lokaci ba wajen amincewa da wannan shawarar saidai kurege ne kadai. Me in haka rijiya domin wani ya amfana? inji shi badai ni ba domin bana bukatar ruwa domin haka mai zai sa na gina rijiya.? Manyan dabbobin sai suka ce in baka shiga aikin gina rijiyar ba to fa ba zaka sha ruwan ba. Wannan sai yayiwa kurege dadi yayi kwanciyar sa yadda yake so, yayinda saurasn dabbobi suka dukufa kan aikin gina rijiya. Sukayi ta hakan kasa ba dare ba rana sannu kan hankli rijiya sai zurfi takeyi kwana da kwanaki. Wata rana masu hakar rijiyar suka iso sai suka samu hakar su ta cimma ruwa domin ruwa ya cika makil sai murna.

Bayan aiki tukuru da dabbobin sukaayi kuma sukaayi nasara, sai suka kuduri aminyar cewar malalacin kurege da yaki aiki ba zai taba ruwan nasu ba, kana shawarta nada daya daga cikin su domin ya rika gadin rijiyar dare da rana. Damisa wanda take ban tsoro daga halittar ta tace zata fara yin gadin rijiyar domin duk wanda lya ganta sai ya tsorata Fari dai sai kara tsanani yakeyi dukkan fadamu da koramai sai dada bushewa sukeyi. Har ta kai ga ragowar fadamar dake da ruwa ita ma ta bushe. Kurege yaga babu wurin samun ruwa saidai rijiyar nan da dabbobi suka gina. Kuma yace tilas ne ya sami ruwan da zai sha. Yayi ta sintiri a lyankin da rijiyar take amma sai yaga akwaai mmai gadi.

Yayinda sauran dabbobi suka gana kurege ya yaudari damisa har ya sha ruwan su sai dasmisa taji kunya. Sai aka zabi kura da tayi gadin rijiya, domin suna gani tana da wayoon da ba zata yarda kurege ya yaudare ta ba. Amma dda maraicen ranar sai kurege ya sake zuwa da zuma gun kura. Saboda kwadayi ita maa ta yarda kurege ya yaudare ta da zuma har ya daure mata hannu ya sha ruwa yayi wanka duk a rijiyar tasu. Sai kunkuru yazo yace zaiyi gadin rijiya. Sauran dabbobi sukayi ta mamaki inda suke cewa yanzu saka iya yin wani abu inda damisa da kura suka kasa? Me zaka iya yi? Yace adai bashi dama, sai dabbobin suka ce to mun baka.

Nan da nan kunkuru ya dagira ya kira matar sa don ta taimaka masa. Sai suka tafi gid itaacen karo tra dibi karko ta shafa a duk jikin kunkuru ta ko ina. Sai kunkuru yayi murmushi da ganin haka, kana ya kkoma bakin rijiya. Ya gina karamin rami inda lya sanya kafafun sa da kansa ciki yabar sai bayan sa kawai. Yla yazamana kamar dutse ne kawai. Lokacin da kurege yazo bakin rijiya sai yaga babu mai gadi yayi dariya kamar cikin sa zasiyi ciwo, yace ai nasan za ayi haka, domin zanlyi amfani da rwawn kamar yadda nakeso. Domin kuwa basusan halin kurege ba ne ainine sarkin wayo inji shi. Kurege ya dirki ruwa a rijiya kamar yadda ransa ke so yalyi wanka kana yayi alkafura. Bayan day gama sai yafito domin nema wurin da zai tsaya ko ya zauna domin ya tsane a rana.

Con ya ga bayan kunkuru sai yace ah ga ma dutse kusa dake jira na zauna kan sa. Domin haka sai kurege ya zauna kan balyaan kunkuru dake da kasro har sai da ya bushe. Ylayinda zai tashi zuwa gida sai yaji abu lya kama shi. Sai yace menene haka ya rike yayi kokari domin kubucewa daga inda yake zaune amma ina dankon karo ya kama shi gam. Yayindda kunkuru ya ga lallai kurege ya kamu sai ya tazso daga cikin ramin, ya fara tafiya inda lyake cewa kurege yau kan Allah Ya kama ka. Sai kazo muje dakai. kunkuru yayi farin ciki da nasarar da ya samu.

Kurtege ya san lallai ya shiga hannu, sai yayi ta maza yace da kunkuru gara ka barni na lafi. Domin ba kasani ba hannu na na dama na da karfi ina iya yiwa dundu a baya har na fasa beyan naka caka-lcaka. Sai kunkuru yace bugi. Kurege ya daga hannun sas na dama ya daoki bayan kunkuru sai hannu ya makale. Yace kuncuru hannu na na hagu yafi na dama yafi na hagu karfi zan doka kama, yace doka, ya kkoka sai hannu ya makale a bayan kunkuru Kurege yace kunkuru kafa ta ta hagu tafi hannun karfi zan doka maka a baya. Kunkuru yace doka ba komai,sai kurege ye doka kafar sa a bayan kunkuru,sai kafa ta manne a baya. Haka kuma ya doka kafar sa ta hagu ita ma ta manne a bayan kunkuru shidai sai tafiya yakeyi da kurege. Kunkuru dai yayi ta tafiya da kurege a bayan sa makale har zuwa ga shugabanin dabbobi,domin yi masa hukuncin da ya kamace shi.
*Shangani/Folktale*

**Karin Magana** **51 Sec.**

Munsha jin yadda Adamu da Hauwa'u suka bar cikin aljanna zuwa duniya. Haka kuma tunda muka fara rayuwa a tsaye muke tafiya....kuma muna kyautata zato watan-wataran zamu bace daga wannan duniya. Watakila bacewa ba itace kalmar da ta dace ayi amfani da ita ba. Domin in har mun bar wannan duniya babu wani'wuri da zamu sake bulla kuma kamar yadda Adamu da Hauwa'u suka bulla cikin wannan duniya. Babu wata duniya dake makale a sama wanda zamu koma bayan mun bar wannan duniyar. Ita dai wannan duniyar kyakkyawa mai kuma cike da hatsari itace kadai muke da ita.
*Gerald Durrel*

**Sau Nawa Kudan Zuma Keyin Zuma A Shekara?** **1min. 28sec.**

Kudan zuma nayin zuma ne yayinda itatuwa ke fidda furanni. Yayinda kudan zuma ke diban wani irin ruwa mai zaki daga furanni,haka kaka kuma kudan zuman ke daukar kwayoyin tsirrai daga wannan fure zuwa wancan. Itacen da yafi bada zuma mai kyau a gabashin Afrika shine wanda ake kira MUTUNDO haka kuma ana kiran sa MUCHESA wanda yakeyin fure daga watan Maris zuwa na mayu. A wasu kasashen Afrika misali itatuwa nayin furanni ne tsakanin watan Disamba zuwa Fabrairu dakuma tsakanin watan Maris zuwa Mayu. A Zambia ana samun zuma ne a lardin Mwinilunga,daKambompo dakuma Zambezi dake sashin arewa maso yammacin kasar. Wadan nan sune yankunan da ake samun zuma tun kaka da kakanni kuma nan ne ake cinikin zuma sama da shekaru 150. Zuma na daya daga cikin abinci mafiya dadi dake samu daga Allah. Ka san yadda kudan zuma keyin zuma? Kudan zuma ne kadai ke yin zuma. Suna daukar digon ruwan NECTA a bakin su da wasu abubuwa na musamman da Allah ya basu,sai suyi ta furawa sai zuma yayi ta fita.

*Chongololo*

## Abubuwa Mau Amfani

**Alkalia Amurka Ya Hana Saran Itatuwa, Domin Kare Kifi** **51sec.**

Wani alkalin tarayya a kasar Amurka kwanan nan ya yanke shawarar da zai dadadawa wanda zaai amfana da batun rai. Cikin watan jiya wani alkali a Seattle dake washington ya dakatar da cinikin katako daga gandun dajin tarayya dake bakin kogin Umpqua dake arewa maso yammacin kasar bisa dalilin cewa gwamnati ta kasa yin la’akari kan ko sare itatuwan katakon zaiyi lahani ga kifafen dake cikin kogin. Me wannan ke nufi? Yana nufi kenan yanzu gwamnati zata sake komawa baya komin bin umurnin kotu. Tilas tayi cikakken bincike kan irin hanyoyin da suka dace ta hanyar aiyukan kula da muhalli wanda a karshe gwamnatin ba zata rika sare itatuwan katakon barkatai ba.

*ENN.*

**Sabuwar Kawan Domin Yakar Sassaucin Cinikayya** **1min. 5sec.**

Yanzu haka an shata layi a yashi domin yaki da dokar cinikayya ya duniya wadda ta sanya kasashe masu tasowa da matalauta cikin kunci ainun. Kungiyar cinikayya ta duniya wanda itace mafi girma da karfi kan cinikayya a duniya tasha samun suka kan yadda take tursasawa jama’ar dake kasashe masu tasowa wanda a sakamakon haka take tilas ta musu dogaro kan dan albarkatun su da baitaka kara ya karye ba. Yanzu kungiyar ta WTO da sassaucin cinikayya suna karfafa yin kawance a dukkan fannoni. Kungiyoyin kwadago dana kare muhalli a Amurka sun bada sanarwar kafa kawance danufin yakar tsarin sassaucin cinikayya. Babban abin sha’awa anan shine domin kungiyoyin dana muhalli sune ke sahun gabe wajen kare albarkatun kasa.

*ENN.*

**Sabbin Halittu Zun Zama Faraki** **1min . 5sec.**

Yau shekaru da dama kenan masana kimiya sukayi imnin cewar akwai kafafun tekuna a duniyar Mars. Domin tabbatar da haka da sauran tunanin su game da duniyar Mars hukumar binciken kimiya ta Amurka (NASA) ta tura wani kumbo domin yayi mata bincike a shekarun 1970. Abubuwan da kumbo ya dawo dasu daga Mars yaso ya tabbatar da wanna tunani da masana kimiyar keyi. Hotunan sun nuna dacan anyi wasu manyan tekuna da suka rufe sashin arewacin duniyar ta Mars.domin sun nuna hotunan da sukayi kama da hakan. Sabbin hujjoji sun nuna wannan tuini ba gaskiya bane. Kamar yadda sakamakon binciken da aka gudanar ya nuna a watan Oktoba,wanda akayi da kwararun kayan aiki ya nuna babu irin wannan layukan ruwan tekun.

*ENN.*